**Farfesa Ibrahim Abubakar ne ya lashe Kyautar Roux Ta 2023**

**SEATTLE, Wash. 10 ga August, 2023**–Babban jagoran lafiya na duniya, Ibrahim Abubakar, ne wanda ya karɓi Kyautar Roux ta 2023, saboda sadaukarwarsa ga bunƙasa samar da ingantacciyar lafiya cikin shekaru talatin da suka wuce.

Yanzu shekara ta 10 ke nan, Kyautar Roux ke zaƙulo ɗaiɗaikun mutane a duk faɗin duniya waɗanda suka samar da bayanan lafiya domin bunƙasa lafiyar mutane. Cibiyar Kididdigar Lafiya [wato Institute for Health Metrics and Evaluation, IHME, a Turance] da ke Tsangayar Karatun Likitanci ta Jami'ar Washington ce ke ba da Kyautar Roux.

"Farfesa Abubakar ya kasance jajirtacce sosai wajen ba da gudummawa ga lafiya a duniya. Ƙwarewarsa da nuna goyon bayansa sun yi tasiri kaitsaye ga aiwatar da ƙudurori da kuma rayukan miliyoyin mutane," in ji Dr. Chris Murray, Daraktan IHME. "Farfesa Abubakar yana da haƙiƙanin abubuwan da Kyautar Roux ke buƙata: ƙirƙira, manufa, da haɗin guiwa. Harkar lafiyar al'ummar ta girmama sosai saboda gudummawar da yake ci gaba da bayarwa da kuma jajircewarsa wajen kawo sauyi."

Babbar nasarar da Farfesa Abubakar ya samu ita ce aikinsa na baya-bayan nan a kan *The Lancet* Hukumar Nijeriya, wanda ya kai Nijeriya ga samar da sabuwar doka da ta buƙaci samar da inshorar lafiya da ƙirƙirar asusun tallafa wa marasa galihu kusan mutum miliyan 83. Ya jagoranci tawagar masu horarwa ta ƙasa-da-ƙasa a watan Maris 2022, inda ya kammala cikakken sharhi a kan tsarin lafiya na Nijeriya ta amfani da bayanan Global Burden of Disease (GBD). Binciken ya gano wagegen giɓin da ake da shi sannan ya ba da shawarwari a muhimman ɓangarori domin inganta aikin kiwon lafiya, tsare-tsaren sadarwa, da kuma samun dama ga kiwon lafiya ga dukkan 'yan Nijeriya.

"A kowace rana, na yi amanna cewa za mu iya kawar da nuna bambance-bambance a sha'anin kiwon lafiya da samar da dama ga kowa ga kiwon lafiya, idan muka yi aiki tare domin inganta rayuwa da yanayin da marasa galihu daga cikinmu suke ciki," in ji Farfesa Abubakar, Shugaban Tsangayar Kimiyyar Lafiyar Al'umma da ke Jami'ar Kwaleji ta Landan.

Farfesa Abubakar ya gaji ƙoƙarin da yake da shi ne na ganin an yi adalci daga mahaifinsa, wanda aka haifa a arewacin Nijeriya, ɗaya daga cikin yankuna mafi fama da talauci a duniya. Mahaifinsa ya yi rayuwa cikin talauci a ƙarƙashin 'yan mulkin mallaka na Burtaniya, amma duk da haka ya yi ilimi, ya kuma gina rayuwarsa a matsayin ma'aikacin gwamnati. Lokacin da yake yaro, Farfesa Abubakar ya ga bambanci na rayuwa da tattalin arziki a ƙasarsa ta hanyar aikin babansa. Lokacin da ya girma, Farfesa Abubakar ya zaɓi ya yi karatun likitanci a arewacin Nijeriya domin magance rashin daidaito a ɓangaren kiwon lafiya.

"Aikina ya sauya kaitsaye zuwa ga lafiyar al'umma bayan na gano irin tasirin da cutar HIV da sauran cututtuka masu yaɗuwa ke yi ga marasa lafiyan da nake dubawa. Lokacin da nake matashin likita, nakan tuna yanayin da marasa lafiya ke zuwa sashena suna mutuwa a kan cutar da ake iya warkewa ta sanƙarau. Mafi yawan waɗannan marasa lafiya matalauta ne sosai sannan al'umma sun kasa taimaka musu," a cewar Farfesa Abubakar. "Na yi imanin cewa, nasarorin da nake samu da jajircewata ga aikin likita da lafiyar al'umma suna da dangantaka da abubuwan da na gani a tsawon rayuwata: abin da yake yiwuwa na matakan samun nasara da dukiya da kuma rashin adalci na sakamako."

Farfesa Abubakar ya kasance jigo ga samar da ci gaban lafiyar ciwon tarin fuka (TB) da cutar COVID-19. Lokacin da yake shugaban sashen masu kula da cutar TB a ɓangare Lafiyar Al'umma ta Ingila a 2015, ya samar da wani shirin bincike wanda ya inganta tantancewa.

Farfesa Abubakar ya kuma shugabanci kwamitoci, kamar Kwamitin Ba da Shawarwari a kan cutar TB na WHO, wanda daga shekarar 2015 zuwa 2018 ya jagoranci gwaje-gwaje mafi kyau da kuma ƙara samar da dama ga yin magani, wanda ya ba da gudummuwa wajen rage kashi 2% na ƙaruwar sababbin masu cutar TB a duniya.

A 2020, an zaɓi Farfesa Abubakar a matsayin mai ba da shawara a kan lamurran Kimiyya da Ƙwarewa a Kwamitin Shugaban Nijeriya game cutar COVID-19. Ya shirya tawaga wadda ta dinga samar da bayanai na shaida, da taimakawa wajen samar da lokutan hana zirga-zirga a ƙasa saboda cutar COVID-19, sannan kuma ya rubuta fiye da maƙala 40 na tsare-tsare, waɗanda suka kasance tsare-tsaren riga-kafi na ƙasa. Ya kuma jagoranci nazarin ƙasa-da-ƙasa na nau'ukan cutar COVID-19, wanda ya ƙunshi masana daga nahiyoyin Turai, Amurka ta Kudu, Afirka, da kuma Asiya.

"Na yi sa'a a kan cewa aikina da matsayina sun ba ni dama ta samun gatar yin aiki a babbar jami'a a Birtaniya da kuma samar da tsare-tsaren lafiya a ƙasar da ta rene ni, da kuma samun damar ba da gudummuwar da ta yi tasiri ga rayuwar al'umma da tsare-tsaren lafiya a duniya da Afurka, musamman ma Nijeriya," in ji Farfesa Abubakar.

A matsayin wanda ya lashe Kyautar Roux, Farfesa Abubakar zai karɓi ladan $100,000 domin ƙarfafa ƙoƙarinsa na taimaka wa tsarin lafiya a Nijeriya da yankin Sahel na Afirka, domin amfanar da wasu daga cikin ƙasashen duniya mafiya talauci, da sauran wasu muhimman shirye-shiryen lafiya na duniya. Za a girmama shi a bikin ba da kyauta a ranar 12 ga Oktoba a birnin Landan.

IHME za ta karɓi sunayen waɗanda aka zaɓa domin lashe Kyautar Roux ta 2024 a watan Satumba. Akan karɓi sunayen waɗanda aka zaɓa ne daga ko'ina a duniya, sannan za su iya kasancewa ma'aikata a ma'aikatun gwamnati, masu bincike a cibiyoyin bincike, 'yan sa-kai daga ƙungiyoyi masu taimako, ko masu ayyukan kiwon lafiya a cikin al'umma.

Domin yin tambayoyi game da kyautar, tuntuɓi info@rouxprize.org.

Domin tattaunawa da kafafen yaɗa labarai, tuntuɓi media@healthdata.org

**Game da Kyautar Roux**
Mamban da ya samar da hukumar IHME, David Roux ne ya ɗauki nauyin Kyautar Roux tare da matarsa Barbara, sannan suke zaƙulo mutane a faɗin duniya saboda ƙirƙirarsu da tasirantuwarsu wajen amfani da bayanan Global Burden of Disease.

**Game da IHME**
Cibiyar Kididdigar Lafiya [wato Institute for Health Metrics and Evaluation, IHME, a Turance] ƙungiya ce mai zaman kanta da take Makarantar Karatun Likitanci ta Jami'ar Washington, wadda take bincike a kan sha'anin lafiya a duniya. Tana samar da manyan matakai na gano muhimman matsalolin lafiya na duniya. Sannan tana gano hanyoyin da ake amfani da su domin magance su.IHME tana jajircewa wajen aiwatar da tsare-tsare ba tare da rufa-rufa ba da samar da wannan bayani ga kowa da kowa, saboda masu samar da tsare-tsare su samu shaidar da suke buƙata domin ɗaukar matakai na rarraba abubuwan da za su inganta lafiyar al'umma. Domin ƙarin bayani, ziyarci healthdata.org.